# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na biyar: Kogi da macizai


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Nkoji C. Muhoho |
| Wanda ya tace: | Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Kabir Isa Jikamshi |


**’Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Mariya: | ’yar shekara 43 |
| Bilkisu: | ’yar shekara 40 |
| Hadiza: | ’yar shekara 15 |
| Adamu: | ɗan shekara 36 |
| Sama’ila: | ɗan shekara 17 |

**MAI GABATARWA:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” a kan kiwon lafiya da kuma yadda za a nisanci kamuwa da cutar gudawa. Sama’ila dai ya auna arziki kamar yadda kuka ji a shirin da ya gabata, da ƙyar ya tsira da ransa. Kun kuma ji yadda Dokta Husaina ta shafe lokaci tana yi wa Hadiza da Sama’ila bayanai game da taƙamaiman abin da ake nufi da cutar gudawa da kuma abin da ke haddasa ta. Ku ba mu aron kunnuwanku domin jin yadda shirin na yau zai kasance.

**Fitowa ta 1: A hanyar zuwa wani rafi**

Mariya, Bilkisu

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Bilkisu, yana da kyau ƙwarai da har za mu sake yin wannan abin. Domin kuwa an daɗe rabon da mu zo rafi tare ɗibar ruwa. |
| **BILKISU** | Na sani, Mariya. Ina jin cewa a ’yan kwanakin baya na yi fama da tarin matsalolin da suka sa na riƙa zama cikin gidan. Abin da ya faru ga jinjirata Fati da kuma rashin lafiyar Sama’ila su suka tauye ni. Daga nan kuma… |
| **MARIYA** | Na sani. Na sani ƙawata, mutuwar Fati babban rashi ne, kuma hakan ne ya sa a yau na ce bari in fito da ke daga cikin gida ganin haka zai iya taimaka ƙwarai ga lafiyarki. |
| **BILKISU** | Ke ƙawata ce ta ƙwarai, Mariya. Ko da yake wasu lokutan kina yin abu kamar wadda ta taɓu. Amma ke abokiyata ce ƙwarai. |
| **MARIYA** | Af! Ina yaran nan suke? Ya kamata a ce suna nan kusa da mu fa. Ina fata dai wannan ɗan naki, Sama’ila, ya san cewa, ’yata ba ƙanwarsa ba ce. |

**BILKISU** Kawata, kina takura musu sosai. Yara ne fa kawai. Shakka babu, Sama'ila yana buƙatar hutawa saboda a shekaran jiya aka sallamo shi daga asibiti.

**MARIYA** Haka ne fa, shi ma yana buƙatar shan iska! Yanzu bari mu gangara rafi mu cika bokitanmu da ruwa.

**BILKISU** Mene ne wannan? Irin ruwan da shanu suke sha, shi ne mu ma za mu yi amfani da shi?

**MARIYA** Ni ba shanun nake tsoro ba ma, waɗancan yaran da ke can wurin.

**BILKISU** Su wane ne? Sama'ila da Hadiza? Ba na hangensu.

**MARIYA** A'a! A'a, waɗanda ke can wurin, Bilkisu. Suna wanka da kuma wanke tufafi, kuma za ki iya ganin abubuwan da sauran yaran suke yi har bayan-gari suke yi a gefen rafin.

**BILKISU** Assha! Mene ne ya same su? Mutum ya taho tun daga wani wuri zuwa bakin rafi, domin kawai ya mayar da wurin banɗaki? Saboda me suke yin haka?

**MARIYA** Wannan shi ne irin dalilin da Sama'ilanki ya yi amfani da shi, inda ya ce yana zuba wa lambuna taki kyauta.

**BILKISU** Haba Mariya, hakan bai dace ba.

**MARIYA** To, ya yi haka. Ko dai mu dakatar da su, ko kuma kawai mu dakata har sai ruwa ya wanke dagwalon. Daga nan, sai mu ɗebi ruwan.

**BILKISU** To amma, ko kin san tsawon jiran da za mu yi a nan? Dubi, yaran suna da yawa, kuma wasu na ci gaba da zuwa wurin.

**MARIYA** To! Ya yi! Ba su buƙatar a ce musu su tashi daga wurin. … Kai, kai! Ku bar wurin nan! Ko ba ku ga nan muke ɗibar ruwan shanmu ba? Ga ni nan zuwa, kuma idan na kama ku zan zane ɗuwawanku da wannan bulalar… har sai…

**BILKISU** *Ha ha ha!* Mariya, Mariya! Kai, kin ba ni dariya!

**MARIYA** To, mene ne kuma abin dariya? Babu wani abin burgewa ko ban mamaki, ga yara suna yin bayan-gida a cikin ruwan da muke sha, kuma muke amfani da shi wajen dafa abinci. … Ina jin daɗi in ga kina murmushi, ƙawata. An daɗe ba a ga haka ba. Cutar gudawa ta shafe wannan annurin daga fuskarki.

**MAI BA DA LABARI:**
An halitta mu ta yadda za mu riƙa kare kanmu daga irin wannan ƙazanta da ke fitowa daga jikinmu. Wannan wani babban bambanci ne a tsakanin mutane da dabbobi.

**Fitowa ta 2: A gefen rafi**
Hadiza, Mariya, Bilkisu, Sama'ila, Adamu

**HADIZA** Wayyo Allah, jama'a! Ku taimaka! A taimakaaaa!

**MARIYA** Haba, a'a, Hadiza ce! Hadiza, Hadiza! Ina zuwa? Zo, zo! Me ya faru?

**BILKISU** Hadiza! Ina Sama'ila? Ina kika baro Sama'ila?

**HADIZA** Maciji! Wani ƙaton macijiiii! Ku taimaka!

**MARIYA** Maciji? Babu macizai a wannan yankin. Yana ina? Ina macijin yake?

**BILKISU** Ina Sama'ila?

**MARIYA** Hadiza, ina Sama'ila? Ina kika ga wani maciji?

**HADIZA** Sama'ila yana tare da macijiiii!

**MARIYA da BILKISU** Mene ne?

**HADIZA** Maciji yana tare da Sama'ila!

**MARIYA** Ikon Allah! Hadiza, don Allah ki yi magana mai ma'ana mana! Kwantar da hankalinki! Yauwa, numfasa, numfasa! Ina Sama'ila? A ina kuka ga macijin?

**HADIZA** Mun yi tattaki da ni da Sama'ila. Ya ce cikinsa yana ciwo. Sai ya je… zuwa… cikin daji… domin ya yi… kin gane ko?… abin nan… daga nan sai na ji ihunshi…

**BILKISU** Saboda me, mene ne ya faru? Sama'ila yana lafiya kuwa?

**HADIZA** Wani maciji ya fito daga… daga… kin gane ko?… daga cikinsa… wani irin… tabɗi!

**BILKISU** Ina Sama'ila yake? Hadiza, yanzu a ina Sama'ila yake? Ina kika baro shi?

**HADIZA** Yana tare da maciji a cikin daji.

**MARIYA** Haba, abin begena. Har yanzu muna cikin duhu. Bilkisu, bari mu tafi nemansa.

**SAMA'ILA** Babu buƙatar ku tafi nemana. Ga ni nan, Mama.

**BILKISU** Sama'ila, mene ne haka? Me nake ji game da macizai?

**SAMA'ILA** Mama, ina da abubuwan da suke kama da macizai a cikin cikina.

**MARIYA** Saurayi kamarka kana wani siddabaru. Hadiza, ina hana ki… m'm mts!...

**BILKISU** Duba, Adamu ne, ɗan'uwan mijina.

**HADIZA** Uncle Adamu!

**ADAMU** Sannunku, yaya kuke? Da ma kuna nan, na je gidan ba kowa?

**MARIYA** Na fitar da Bilkisu daga gidan can domin ta sha iska. A taƙaice, muna buƙatar ruwa mai tsabta… uhmmm… idan za ka iya kiranshi ruwa mai tsabta.

**ADAMU** Sama'ila, na fahimci cewa yanzu kam ka murmure sosai, fiye da da.

**MARIYA** Ya sami sauƙi sosai, amma a gaskiya ba shi da lafiya. Yana fito da macizai daga cikin cikinsa. Wane irin magani kuka ba shi a asibiti? Ina tsammanin cewa, ka san abin da kake yi a matsayinka na ma'aikacin kiwon lafiya.

**ADAMU** Kashin macizai? Sama'ila, me ya faru? Yaya na ga ka yi shiru? Me yake faruwa ne?

**SAMA'ILA** Kawu, wasu… wasu irin macizai ƙanana suka fito daga… daga… ka dai gane…

**ADAMU** *Ha ha ha!* Kada ka damu! Tsutsotsin ciki ne kawai. Suna fitowa ne bayan da aka nakasa su. Maganin da aka ba ka ke nan a asibiti.

**MARIYA** Kana nufin, yanzu kuma kuna kiwon tsutsotsi a cikin 'ya'yan hanjin mutane?

**BILKISU** Ɗana ya sake kamuwa da rashin lafiya ne? Ba zan iya jurewa wata rashin lafiyar ba a cikin iyalina. Ni kawai ba zan iya jurewa ba.

**ADAMU** A'a, a'a! Kada ki damu, Bilkisu! Sama'ila ya yi fama da cututtuka guda biyu. Cutar gudawa mai tsanani da kuma raɗaɗin da ya yi fama da shi. Wata ƙaramar ƙwayar cuta ce da ake samu a cikin ruwa, ko a doron ƙasa, ko kuma cikin iska, ta haddasa shi. Yin fama da irin waɗannan cututtuka a kai-a kai yakan haddasa matsanancin ƙarancin ruwa a cikin jiki ko kuma a rasa rai. Amma yanzu, an kuɓutar da Sama'ila daga wannan hatsarin.

**MARIYA** To, idan haka ne, saboda me yake yin kashin tsutsotsi? Ko ba ka ga yadda waɗannan yara suka razana ba ne?

**ADAMU** Ina sake nanata miki, bai kamata ki damu ba a halin yanzu. Sama'ila ya yi fama da wata ƙwayar cuta ta biyu, wadda kusan game-gari ce. Ba a san yadda ƙwayoyin tsutsar suka shiga cikin cikinsa ba, har suka gawurta suka zama macizan ciki. Amma yanzu bayan da ya sha magani, ba su da sauran

wata mafaka da za su girma a cikin cikinsa, ko kuma cikin 'ya'yan hanjinsa. A dangane da haka ne suke neman hanyar fitowa daga ciki, inda sukan biyo bayan-gida, su yiwo waje tare.

**BILKISU** Ta yaya Sama'ila ya haɗiye waɗannan tsutsotsin? Shakka babu, sun samu shiga cikin cikinsa ta bakinsa ne. Ba ma cin tsutsotsi a gidanmu!

**MARIYA** Adamu, ka rikita mu da irin ilimin da ka koya. Ya kamata ka yi bayani sosai.

**ADAMU** Ai, suna shiga cikin ciki ne a matsayin ƙwayaye ko kuma ta cikin kayan lambu. Yanayin hanji, wuri ne mai kyau da za su iya yin girma.

**MARIYA** Idan haka ne, Malam Alhudahuda, ta yaya ƙwayayen suke shiga cikin kayan lambu, ruwa, da sauransu? Wane ne kuma yake sa su?

**ADAMU** Sama'ila, a ina da kuma yaya ka ga waɗannan tsutsotsi? Ina nufin waɗanda suka fito daga cikin jikinka.

**SAMA'ILA** Kawo! Ina… ina… ka dai gane...

**HADIZA** Yana bayan-gida a cikin daji.

**ADAMU** Wannan ita ce amsarku!

**MARIYA** Kin gani! Kina gani ko Bilkisu? Mene ne na faɗa miki game da ɗanki da kuma halayensa na… mhmm… na zuba takin gargajiya a cikin lambunan jama'a?

**BILKISU** Mariya, ki daina matsa wa fa ɗana!

**MARIYA** Ba haka ba ne! Ina dai kawai….

**ADAMU** Ku dakata ku biyun dukanku! Bilkisu, kin tambaya game da yadda ƙwayayen suka shiga cikin jikin Sama'ila. A taƙaice, sun shiga ne a can cikin dajin inda ya yi bayan-gidan. Kuma ya juye isasshun ƙwayayen da za su sa dukan al'ummar

ƙauyen nan su iya yin fama da tsutsar ciki da kuma cutar gudawa.

**SAMA'ILA** Assha! A'a, wayyo! Ku gafarce ni, ba na nufin na… ban sani ba… don Allah ku yafe min!

**ADAMU** Ba laifin Sama'ila ba ne. Lokacin da ya yi fama da gudawa da tsutsotsin ciki, wasu ƙwayoyin cuta suka haddasa masa ne. Bai kuma san cewa, bayan-gidan da ya riƙa yi, zai iya sa sauran mutane su harbu ba.

**MARIYA** To laifin wane ne? Kamata ya yi, su ma ma'aikatan asibiti a aza musu laifi, saboda ya kamata su yi mishi magani.

**ADAMU** Ina da tabbas a kan abu guda, Sama'ila yana murmurewa sosai. Tsutsotsin suna fitowa, saboda yanzu an yi magani a wurin da a da suke fakewa, har su girma a cikin cikinsa. Yanzu ba za su iya ci gaba da girma ba, suna mutuwa. Amma akwai buƙatar mu ilimantar da dukan al'ummar yankin nan game da waɗannan abubuwa.

**MARIYA** Musamman ma waɗancan yaran waɗanda suke yin bayan-gida a cikin rafi. Da masu shayar da shanu, da 'yan wanki da kuma… uhmmm… Ina mamaki duk da haka, dukanmu ba mu kamu da cutar gudawa ba.

**ADAMU** Yanzu kam, kun fahimci lamarin. Dukanmu, muna cikin hatsari. Wasu lokutan, mu ne maƙiyan kanmu da kanmu. Wannan ne ya sa ya kamata mu samu ƙarin ilimi game da hanyoyin yin rigakafin kamuwa da cututtuka.

**MAI GABATARWA:**

Akwai abubuwa masu yawa da za a iya koya game da yadda ake iya yaɗa cutar gudawa. Ga alama za a iya kauce wa yawancin hanyoyin samun cutar idan jama'a suka riƙa kula da junansu. Za ku iya kai ziyara a shafinmu na

yanar gizo mai adireshin www.dw-world.de/lbe, domin sake sauraron wannan shirin ko kuma aiko da tsokaci.